**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.11 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Ɓurɓushin Musulunci A Waƙoƙin Baka na Hausa: Nazari Daga Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Halima Isma'il,**
**Aisha Aminu Yahya**

Sashen Koyar da Hausa, Tsangayar Harsuna, Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano State

**Corresponding Author: Halima Isma'il**

***Tsakure***
*Kiɗa da waƙa na ɗaya daga cikin hikimomi da fasahohi da al'umma kan zaɓa ta tafiyar da rayuwarta cikin jin daɗi da annushuwa a kansu. Makaɗan baka na Hausa shahararrun makaɗa ne waɗanda suke shirya waƙoƙinsu a kan manufofi da matakai daban-daban. Waƙoƙi baka suna ƙunshe da manya da ƙananan saƙonni waɗanda ake ƙoƙarin cusa saƙonnin cikin zukatan masu sauraro.* Gusau (2012, sh. 219) ya bayyana cewa waƙa wata aba ce wadda ake aiwatarwa a cikin harshe mai jan hankali tare da ba da damar yin tunani da kuma yin lura. Waƙa ta zama wata hanya ta sadarwa da tunani zuwa ga mazaunar al'umma a zanguna daban-daban da rayuwar jama'a takan shuɗe a kansu. Haka kuma ya bayyana cewa, a kowace al'umma a duniya akwai wani tsari da take amfani da shi wajen shiryawa da aiwatar da waƙoƙi domin tabbatar da maslaha cikin nasiha da faɗakarwa da samar da walwala a rayuwa. Gusau (2014,sh,1) ya kalli waƙar baka da cewa: wasu kalmomi ne na ƙulla da amsa da ƙari da azanci da kuma shirya kalmomi waɗanda suke nuni a kan matakai na bayyana waƙar baka ta Hausa. Manufar wannan *takarda ita ce a fito da yadda maƙaɗi Kassu Zurmi yake amfani da wasu hikimomi wajen ƙulla zubi na waƙoƙinsa ta yin amfani da nassi da hadisai a wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙinsa. Wannan ne ya sa aka ga dacewar bibiyarsu da nufin yin taƙaitaccen tarke a kansu.* Wannan aiki an ɗora shi ne a kan ra'in Kawanci/ƙawa (Aesthetics theory)

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Kiɗa da waƙa al'amari ne mai daɗaddɗan tarihi, musamman ta kallon irin zanguna da suka ratso a rayuwar al'umma ta yau da kullum.'Ya'yan Hausawa tun lokacin da suka fara iya magana da fahimtar zance zuwa balaga da samartaka da zango na aure da kafa iyali da manyantaka zuwa tsufa sukan saurari waƙoƙi da makaɗansu na Hausa suke aiwatarwa. Gwargwadon kowanne zango da shekaru na al'ummar Hausawa. Kamar yadda aka bayyana masana da dama sun yi aikace aikace masu tarin yawa a kan waƙoƙi waɗanda suka haɗa da waƙoƙin baka da rubutattun waƙoƙi. Waƙa ta baka da rubutacciya hanya ce ta isar da saƙo zuwa ga al'umma, wadda ta ƙunshi waɗansu ƙa'idoji na rerawa da kari da murya mai zaƙi domin saƙon ya yi saurin isa tare da karɓuwa wajen al'umma.

Gusau (2003, sh. xi) ya bayyana cewa, in dai ana so waƙar baka ta cika ko a kira ta da waƙar baka akwai wasu matakai ko kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma'anar waƙa baka su ne kamar haka, rerawa da hawa da saukar murya da daidaita sautin murya cikin amsa-amon-kari da rauji da azanci da naƙaltar harshe da hikima da fasaha da kiɗa da karɓi ko amshi da gaɗa da tafi.

## 1.1 Manufar Bincike

Manufar wannan takarda ita ce fito da yadda maƙaɗi Kassu Zurmi yake amfani da wasu hikimomi wajen ƙulla zubi na waƙoƙinsu ta yin amfani da nassi da hadisai a wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙin. Wannan ne ya sa aka ga dacewar bibiyarsu da nufin yin taƙaitaccen tarke a kansu.

Wata manufar ita ce bibbiyar waƙoƙin makaɗan Hausa, musamman waƙoƙin Makaɗi Kassu Zurmi ta yadda yake gudanar da su ta tsarin shigar da abubuwa da suka shafi addinin musulunci a waƙoƙin. Haka kuma wannan takarda ta ƙunshi gabatar da bayani a kan gudummawar da waƙoƙin baka na Hausa suke bayarwa ta ɓangaren addini wanda ya ƙunshi kyawawan ɗabi'un Hausawa waɗanda suka dace da Musulunci, da faɗakar da al'umma a kan abin da Allah (SWT) ya umarta a yi da waɗanda ya yi hani da su a cikin ɗiyan waƙoƙin.

## 1.3 Ra'i da Hanyoyin Gudanar da Bincike

Wannan aiki an ɗora shi ne a kan ra'in Ƙawanci/ƙawa (Aesthetics theory) wanda masani irin su Alexandar Baumgarten (1735) da Theodor Adonor (1970) da Oscar Wilde a ƙarni na (19) da sauransu suka samar da ra'in suka kuma yi aikace aikace masu yawa ta amfani da ra'in. Masanan sun ƙiƙƙiro ra'in ne domin su nuna cewa kyau yana gaba da komai. Ra'in ƙawa, "hanya ce da take magana a kan kyau wanda aka yi ƙoƙarin adana fasaha ba tare da la'akari da tarbiyya, ko aƙida ko kuma dalilan siyasa ba" (Baldic, 2004:3).

## 1.4 Hanyoyin Gudanar Da Bincike

Matakan da aka bi wajen gudanar da wannan aiki shi ne samo waƙoƙi waɗanda aka yi amfani da su a wannan aiki waɗanda suka haɗa da tattaro waƙoƙi daga CD-CD da kasakasai daga wurare daba-daban. Haka kuma an yi karance-karance da nazarce-nazarce domin samo bayanai a kan abubuwan da suka danganci wannan aiki.

an nazarci ayyukan da suka gabata masu dangantaka da wannan aiki a ɗakunan karatu mabambanta, musamman waɗanda suka shafi adabin baka na Hausa ɓangaren waƙar baka a matakan ilimi daban-daban, an duba maƙalu da ƙasidu da sauran takardun ilimi. Mataki na gaba na gudanar da wannan aiki shi ne an tattauna da mutane daban-daban waɗanda suke da ilimi a kan waƙoƙin makaɗan baka na Hausa.

## 2.1 Waƙa

Dunfawa (2002) ya bayyana waƙa da cewa, waƙa ita ce abu mafi tasiri ga al'ummar Hausawa musamman wajen isar da saƙo, don haka hankulan masana da kuma manazarta adabin Hausa da yawa sun dogara da waƙa wajen isar da saƙonsu a hikimance a kuma sauƙaƙe. Daunfawa ya ce waƙa hanya ce ta isar da saƙo cikin sauƙi ga al'umma. Haka kuma ya bayyana cewa, akwai abubuwa da dama da masu nazari za su iya nazarin su a waƙa. Wannan dalilin ne ya ja hankali masana da manazarta suka duƙufa domin gudanar da bincike a kan waƙa domin fito da abubuwa da kuma fasahar da makaɗa ke da ita.

Gusau (2003) ya ce: waƙar baka, wani zance ne shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gaɓa –gaɓa bisa ƙa'idojin tsari da daidaitawa a rere cikin sautin murya da amsa amon kari da kiɗa da amshi. Gusau (2003) ya bayyana cewa in dai ana so waƙar baka ta cika ko a kira ta da waƙar baka akwai wasu matakai ko kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma'anar waka baka su ne kamar haka: Rerawa da hawa da saukar murya da daidaita sautin murya cikin amsa-amon-kari da rauji da azanci da naƙaltar harshe da hikima da fasaha da kiɗa da karɓi ko amshi da gaɗa da tafi da zabiyanci da saƙo.

## 2.2 Makaɗan Maza

Masana irin su Auta (1986) da Umar (1987) da Gusau (2003) da Junaidu da 'Yar'aduwa (2007) da Magaji (2016) da sauransu sun bayyana makaɗan maza da cewa, su ne makaɗan da ke yi wa jarumai waƙa domin su nuna gwaninta a fagen jarumta, Waɗannan masana sun bayyana cewa ire-iren waɗannan maza ko jarumai sun haɗa da 'yan dambe da 'yan kokawa da mafarauta da sauransu. Haka kuma sun ƙara da cewa zuga da koɗawa su ne fitattu wajen gina jigogin waƙoƙin maza.

Makaɗan maza makaɗa ne da ke waƙa domin su zuga mutum tare da tunzura shi domin ya yi wani abu na jarumta wanda ba kowane zai iya wannan abin ba sai wanda ya shirya. Waɗannan makaɗa na maza su ne wasu masanan ke kiransu da makaɗan jarumta. Masanin ya ce Waƙoƙin maza su ne waƙoƙin da makaɗan maza ke yi musamman domin su wasa maza, ma'abota ayyukan ƙarfi da jarumtaka. Waɗanda suka haɗa da dambe da kokawa da tauri da farauta, waɗanda suke buƙatar karfin hali da kuma shiri na musamman.Waɗannan al'amura ne na sayar da rai, saboda haka masu yin su suna buƙatar zuga da koɗawa. Masana irin su Auta (1986) da Umar (1987) da Gusau (2003) da Junaidu da 'Yar'aduwa (2007) da Magaji (2016) da sauransu sun bayyana makaɗan maza da cewa, su ne makaɗan da ke yi wa jarumai waƙa domin su nuna gwaninta a fagen jarumta, Waɗannan masana sun bayyana cewa ire-iren waɗannan maza ko jarumai sun haɗa da 'yan dambe da 'yan kokawa da mafarauta da sauransu.

Makaɗan maza makaɗa ne da ke waƙa domin su zuga mutum tare da tunzura shi domin ya yi wani abu na jarumta wanda ba kowane zai iya wannan abin ba sai wanda ya shirya. Waɗannan makaɗa na maza su ne wasu masanan ke kiransu da makaɗan jarumta. Ya ce Waƙoƙin maza su ne waƙoƙin da makaɗan maza ke yi musamman domin su wasa maza, ma'abota ayyukan ƙarfi da jarumtaka. Waɗanda suka haɗa da dambe da kokawa da tauri da farauta, waɗanda suke buƙatar karfin hali da kuma shiri na musamman.Waɗannan al'amura ne na sayar da rai saboda haka masu yin su suna buƙatar a zuga da koɗawa.

## 3.1 Addini

Isma'il (1417) (1997,sh. 9) ya bayyana addini da cewa: addini shi ne ranƙwafawa izuwa wani abu da biyayya izuwa gare shi. Ismail (1997,sh, 9) ya ce addinin musulunci shi ne addinin da Allah (SWT) ya zabo ya kuma yadda da shi, ya kuma yardarwa bayinsa shi, ya

kuma umarce su da su bauta masa da shi. Wannan shi ake nufi da addinin musulunci. Ya ƙara da cewa addinin musulunci ya haɗa abubuwa guda uku akwai Musulunci akwai Imani sai kuma Ihsani. Kamar yadda ya zo a Hadisin Manzon Allah (SAW) a *cikin* Hadisin Jibrilu inda yake tambayar annabi Muhammadu (SAW) inda ya ce:

Ya Muhammadu ba ni labara a bisa musulunci sai Manzon Allah (SAW) ya ce:

> *"Musulunci shi ne ka shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi (SAW) Manzon sa ne, ka tsai da sallah, kuma ka ba da zakka ka yi azumin watan Ramadana, ka ziyarci ɗakin Allah Mai Girma idan ka sami ikon zuwa gare shi.)"*
> *(Muslimu ne ya ruwaito shi)*

Shi ko Jabir Aljaza'iri (1437) (2016:7) ya kalli musulunmci da cewa musulunci shi ne imani da Allah da kuma gasgatawa da shi. Jabir (1437) (2016,sh,7) ya ci gaba da cewa Imani shi ne musulmi ya ba da gaskiya ga Allah ya tabbata da samuwar Ubangiji maɗaukakin sarki ya kuma gasgata cewa ubangiji yana nan . Kuma ya yadda da cewa Ubangiji shi ne ya ƙagi sammai da kassai kuma masanin gaibu. Kuma shi ne Ubangijin komai, wanda ya mallaki komai. Babu wani ubangiji sai shi. Haka kuma Ubangiji ya siffantu da siffofi na cika, kuma Ubangiji ya tsarkaka daga dukkan tawaya. Dukkan godiya ta tabbata gare shi.

Kamar yadda ya zo a cikin hadisi, inda Jibrilu yake tambayar Annabi Muhammadu inda yake cewa:

> *"Sai Annabi ya ce Ka yi imani da Allah, da Mala'ikunsa da littattafansa, da Manzonninsa da ranar lahira, kuma ka yi imani da kaddara (wato alkhairi da kuma kishiyarsa).*
> *(Muslimu ne ya ruwaito shi)*

Umar (1987,sh, 9) Ya bayyana Addini da cewa, hanya ce ta daidaita tunanin ɗan'adam da dukkannin al'amura na rayuwarsa. Addinin Musulunci shi ne addinin da Allah (SWT) cikin rahamarsa, ya albarkace mu da karbar addinin musulunci wanda Allah (SWT) ya ce shi ne kaɗai sahihin addini, kuma shi ne addini karɓaɓɓe a gare shi. Umar (1987sh, 9) ya bayyana ma'anar addini da cewa, hanya ce ta bauta, wadda tilas, dukkan ɗan'adam ya bi.

### 3. 2 Addinin Musulunci a Wurin Al'ummar Hausawa

Masana da dama sun yi aikace- aikace a kan addinin musulunci tare da bayani a kan yadda addinin musulunci ya shigo ƙasar Hausa. Ya zo a cikin tambayoyi da amsarsu da a ka yi a (O.I.C.) University (Wato Jami'ar Musulunci da ke ƙasar Niger (2009/2010) Shafina (2). Mene ne musulunci?

Musulunci: Shi ne miƙa kai ga Allah cikin kaɗaita shi, da miƙa wuya da ɗa'a da biyayya a gare shi da yin watsi da shirka.

Musulunci: Shi ne ƙa'idojin shari'ar da Annabi Muhammadu (SAW) ya zo mana da su daga wajen Allah Maɗaukakin Sarki.

Waɗannan bayanai biyu su ne Musulunci mai rukunai ko ginshiƙai biyar (5) Kamar haka:

1-Tauhidi. 2-Sallah. 3-Azumi. 4-Zakkah. 5-Aikin Hajji.

Abdulkarim Shaharustani (1429 Hijra) wanda ya yi dai-dai da (2008, sh. 571) ya bayyana cewa akwai addinai masu tarin yawa da kuma mabiyansu, alal misali akwai addinin Musulunci da addinin Hindu da addinin bautar Gumaka Yahudanci da Nasaranci da Sabi'anci da Mujusanci da Hannafiyanci da sauransu da yawa. Shaharastani (2008, sh.

571) ya bayyana cewa Allah (S.W.T.) a cikin Alƙur'ani mai mai girma a Suratul Hajj (sura ta 22): Aya ta 17 Allah (SWA) yana cewa:

*Lalle ne waɗanda suka yi imani da waɗanda suka tuba*

*(yahudu) da waɗanda suka karkace (Saba'awa) da*

*Nasara da Mujusawa da waɗanda suka yi shirka,*

*lalle ne Allah Yana yin hukunci a tsakaninsu*

*a ranar ƙiyama. Lalle ne Allah mahalacci ne a*

*kan dukkan kome. (Kur 22 aya 17)*

Shaharustani (1429) (2008, sh. 571) ya bayyana cewa Ihsani kamar yadda ya zo a hadisin Annabi Muhammadu (SAW) wanda Umar ya ruwaito, Ihsani shi ne ka bautawa Allah kamar kana ganin sa in kai ba ka ganin sa to shi yana ganin ka. Wannan shi ne cikar kamala da kuma cikar musulunci, ga wanda ya tsira.

Kamar yadda ya zo a hadisi na biyu inda Jibrilu ya tambayi Annabi Muhammadu (SAW):

*"Ba ni labari a kan kyautayi (Ihsani) sai Manzon Allah (SAW) yace shi dai Ihsani (kyautahi) shi ne ka bautawa Allah kai ka ce kana ganinSa, idan ka kasance ba ka ganinSa, to shi yana ganinka" (Muslimu ne ya ruwaito shi)*

Haka kuma Allah yana cewa a suratul baƙara aya ta 112: Allah ya na cewa :

*Lalle wanda ya miƙa fuskarsa ga Ubangiji*
*(ya musulunta kenan ya kuma kyautata shi*
*shi musuluncin) ladansa yana gurin Ubangijinsa*
*ba tsoro a gare shi kuma babu baƙin ciki ko ɓacin rai a tare*
*da shi.*

### 3.3 Tasirin Musulunci a waƙoƙim Baka na Hausa

Makaɗan baka na Hausa sukan tsara waƙoƙinsu ta hanyar shigar da abubuwa da suka danganci addini Musulunci. Alal, misali Gumel (1992,sh.19) ya bayyana cewa, waƙoƙin baka na Hausa suna ƙushe da abubuwan addini musamman waɗanda suka shafi tarbiyyar Musulunci, saboda mawaƙan Musulmi ne, Haka kuma iyayen gidansu da sauran waɗanda suke wa waƙar da zuriyarsu duk Musulmai ne.

Gumel (1992,19-20) ya yi ƙarin bayani a kan abubuwan da Musulunci ya wajabta wa Musulmai, wanda ya haɗa da tarbiya da sauran hanyoyi na gyaran hali. Makaɗan baka na Hausa sukan jero muhimman abubuwa waɗanda musulunci ya yi umarni da su, ya kuma umarci Musulmai da aikata su, kamar tauhidi da tsoron Allah da cusa begen Annabi (S.A.W.) da koyar da hanyoyin ibada da tarbiyya da mu'amalar jama'a da halin kirki musamman gaskiya da ilimi da adalci da haƙuri da mutunci da zumunci da tsafta da sana'a da hangen nesa da kuma illar ƙarya da shaye-shaye da karuwanci da cin haram da dai sauran miyagun ɗabi'u waɗanda Musulunci ya yi umarni ko hani da su. Waɗannan abubuwa da aka jero makaɗan baka na Hausa sukan tsara waƙoƙi da su, domin faɗakarwa ko isar da saƙo ga al'umma.

### 4.1 Tasirin Musulunci a Waƙoƙim Kassu Zurmi

Makaɗi Kassu Zurmi makaɗi ne mai basira da hikima ta sarrafa harshe, wanda yake sarrafa wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙinsa ta ambaton Allah da manzonsa . Wannan ne ya

nuna mana cewa makaɗi Kassu yana ɗaya daga cikin makaɗa da suke da ilimi na addinin musulunci.

Ga wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙinsa da yake jejjefa kalmomin addinn musulunci a ciki. Misali a waƙar da ya yi wa Adamu Dodo inda yake ambaton sunan Allah a cikin ɗiyan waƙar kamar haka :

**Jagora** :Ajiya dawa ba ajiya ba,
:Kai jama'a ajiya dawa ba ajiya ba,
:Watanga na yanzu.
:Har ajiyad ɗaka ba ajiya ba.
:Sai dai Allah shi kiyaye.
:Kai dai Allah shi tsare ka.
(Kassu Zurmi, Waƙar Adamu Dodo)

A wannan ɗan waƙa da ya gabata makaɗi Kassu Zurmi ya yi amfani da kalmar Allah, inda yake roƙon Allah ya tsare musu kayayyakinsu da dukiyarsu da aka ajiye a wanu waje, domin Allah shi kaɗai ne zai tsare musu ba wani ba.

Haka kuma yana cewa:

Jagora : Tun da kowa amre shi ita ka cishe shi,
:Ta biya kuɗin garin karen kyasko,
: Sannan ta yi mai abin ruhwa,
: Kana ta koma ta yi dabbalin abin ɗamri.
(Kassu waƙar Barau)

A nan makaɗi Kassu ya yi amfani da kalmar aure a ɗan waƙarsa . Aure sunna ce ta Annabi Muhammadu (SAW). Sunnah shi ne duk abin da Manzon Allah ya yi ko ya umarta a yi ko aka aikata kuma bai hana ba. (CNHN, 2006, sh.402) ya bayyana sunna da cewa, abin da Manzon Allah ya yi ko ya yi umarni a yi ko aka yi a gabansa bai tsawatar ba.

Aure sunna ce wacce Manzon Allah (SAW) ya umarci musulmi da su yi domin a haifafa, a sami ƙaruwa ta musulmai.

A wannan ɗan waƙa makaɗi Kassu ya bayyana yadda ta kasance wa Barau a yayin da ya nemi aure. Haka kuma auren ya zama irin abin nan ne na Hausawa da sukan ce Allah ya yi aure da mara kwabo, domin ya sami auren cikin sauƙi, ba tare da kuɗinsa sun shiga ciki ba.

Haka kuma Kassu yana cewa:

Jagora: :Barau Allah yay ma rabo,
:Yay ma babban arziki
:Tun da yay maka mata zaruma,
: Hura cike ba ta hatcinka ba,
:Ka ci tuwo da miya sai ka gaji.
(Kassu waƙar Barau)

A nan Kassu yana ƙoƙarin ya nuna cewa Barau mutum ne wanda Allah ya taimake shi, domin Allah mai jin ƙan bawansa ne. Allah ya yi wa Barau arziki domin ya ba shi mata mai arziki mai kuma kirki, saboda Barau ya yi aure maimakon ya ɗau nauyin matar sai ita ta ɗau nauyinsa. Wannan duk taimako ne daga Allah (SWA) da ya ba shi mata mai tausayi da biyayya.

Ga wani ɗan waƙar kamar haka:

Jagora : Allah ya biya ma Awwal buƙata ɗan Sarki,
: To, daAwwal da Bukka da Amarya,
: Da Ɗanmamu dutci,
: Kwana na bakwai gidan Ɗanmamu,

: Rad da yay man doki.
Jagora : Hura inji Bukka.
:Tuwo inji Bukka,
: Shinkahwa da swahe danama ka karya,
: G kaji a yank eta gyara,
: Allah ya biya ma Bukka buƙata uwag gida
(Kassu waƙar Awwal Ɗan Sarki)

A wannan ɗan waƙa Kassu ya yi amfani da kalmar Allah, inda ya yi addu'a ya kuma roƙi Allah da ya biya wa masoyinsa Awwal ɗan Sarki buƙatunsaa tare da matansa musamman Bukka, saboda alkhairin da suka yi masa musamman yadda aka karɓe su a lokacin da suka je gidansa, ga abinci mai rai da lafiya da wajen kwana.

Haka kuma yana cewa

Jagora : Ni na baz zuwa gida ba ka yi shi ba,
: Baba in dai sata ka kai, yi satak ka saye,
: In kau ka gab a ka sata yi hwashe,
:Amman a baz zuwa gida ba ni da shi,
:In kau na isa gidan bilai ya kasan,
:Sai La'ilaha illallahu,
: Daɗa Kassu ya yi rantsuwak kahhwara.
( Kassu waƙar Nomau na magarya)

A wannan ɗan waƙa da ya gabata makaɗi Kassu ya yi amfani da kalmar la'ilaha illallahu, wato babu wani Sarki sai Allah, Allah shi ɗaya ne babu wani abin bautawa face shi. A nan Kassu yana nufin idan aka yi abu mara kyau sai a tuba ga Allah, domin Allah mai karɓar tuba ne.

Haka kuma Kassu yana cewa

Jagora : Rad da Allah yay yo ni,
: Kassu rad da Maisama yay yo ni,
: Ka ganan nan ban zo kiɗa ba sabon birni
: Sai da Ummaru yay kiram mu sabon birni,
: Sanda jikan Shawai,
: Ummaru jikan Shawai,
:Zuriyag gidan Jari Kada.
(Kassu waƙar Ummaru Sabon birni)

A wannan ɗan waƙa makaɗi Kassu ya yi amfani da kalmar Allah da mai sama inda ya nuna cewa Allah shi ne mai halitta, kamar yadda ya kawo a ɗan waƙar cewa rad da Allah yay yo ni, ya kuma ce rad da mai sama yay yo ni. A nan makaɗin ya yi imani da cewa Allah kaɗai shi yake halitta. Haka kuma Allah ne ya halicce shi ya kuma nufe shi da yin waƙa.

### 5.1 Sakamakon Bincike

Kamar yadda aka sani, bincike ba ya yuwuwa ba tare da an samo sakamakon abin da aka binciko ba. Babu shakka a kowane bincike da aka gabatar a ƙarshe akan sami wata manufa da mai binciken ya cim ma. A sakamakon wannan bincike an yi ƙoƙarin gano cewa akan sami ɓurɓushin addinin musulunci a waƙoƙin makaɗan baka na Hausa, kamar yadda aka samu a waƙoƙin Kassu Zurmi. Kassu Zurmi na ɗaya daga cikin makaɗan maza waɗanda suke tsara waƙoƙinsu suke kuma jajjefa nassin Alkur'ani mai tsarki da Hadisan Annabi (SAW) a ɗiyan waƙoƙinsu. Sukan yi hakan ne domin su ja hankalin masoyansu da sauran masu sauraron waƙoƙinsu. Wannan ya nuna cewa waƙoƙin ba kawai nishaɗantar da al'umma suke ba, har ma da ilimantarwa game da faɗin Allah da Annabinsa.

Haka kuma an gano cewa makaɗan musamman Kassu Zurmi suna da ilimi na Addinin Musaulunci daidai gwargwado, wasun su ma sun fito ne daga gidan malamai.

**6.1. Kammalawa**

A wannan takarda mai taken ɓurɓushin Musulunci a Waƙoƙin Baka na Hausa Nazari daga waƙoƙin Kassu Zurmi an yi bayani a kan ma'anar waƙa da yadda ake iya samun ɓurɓushin addinin musulunci a waƙoƙin baka na Hausa, Waɗanda suke ƙunshe da abubuwa da suke da alaƙa da musulunci. Haka kuma an kawo ma'anar addinin musulunci daga masana daban-daban. An bayyana yadda musulunci ya yi tasiri a waƙoƙin baka na Hausa, inda aka kawo wasu muhimmnan abubuwa da suka danganci addinin Musulunci. Wannan takarda ta fito da misalai daga wasu daga cikin waƙoƙin makaɗi Kassu Zurmi, domin ganin yadda makaɗin ya yi amfani da kalmomi na addini a cikin ɗiyan waƙoƙinsa. Daga ƙarshe aka kawo sakamakon bincike sai kammalawa.

**Manazarta**


Amin, M. L. (B.S.) "Bitar Waƙoƙin Baka a Kasar Hausa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu". A cikin *Harshe 3: Journal of African Languages*, Department of Nigerian and African Languages. Zaria: Ahmadu Bello University.

Aljairi, B.J. (2016) *Munhaj Muslim Saudiya*. Maktabatul Bukhari.
CNHN, (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Gusau, S.M. (2002) *Sarkin taushi Salisu Jankiɗi.* Kaduna: Baraka Press.

Gusau, S.M (2008). *Waƙoƙin Baka a Kasar Hausa:* Yanaye-yanayen da Sigoginsu.

Ibrahim M. S.(1976) "Kowa ya sha kiɗa" Takarda ta uku Kano: Jami'ar Bayero

Ismail, M.B. (1417) (1997) *Alfigiru Alwarihu*. Alƙahira-Masar: Darul Mana.

Magaji, A (2016). *Kassu Zaurmi da Waƙoƙinsa,* Ibadan: Spectrum Books Limited.

Magaji, A. (1980)"Nazarin Rayuwa da Waƙoƙin Alhaji Kassu Zurmi". Kundi Digri na Ɗaya, Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeria, Jami'ar Bayero.
Shaharustani, M.A. (1429) (2008) *Milal Wal nihal,* Bairuit Lubnan.

Tahir M. R. (2011). *Tasirin Musulunci a Waƙoƙin Baka na Hausa,Zaria*: Department of African Languages and Cultures,Ahmadu Bello University.

Usman, H. S (2016) "Nazarin Turken Ta'aziyya a Waƙoƙin Dr Mamman Shata Katsina".Kundin Digiri na Biyu Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeria, Jami'ar Bayero.

Zulyadaini, B. Abba, M. (2000). *Nazari kan Waƙar Baka ta Hausa.* Zaria: Gaskiya Corporation Limited.